# Surah 100: Al-Adiyah - سورة العاديات

بسم الله الرحمن الرحيم

[100:0] Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.*

وَٱلْعَـٰدِيَـٰتِ ضَبْحًا ١

[100:1] Ina rantsuwa da dawakai masu saurin sukuwa.

فَٱلْمُورِيَـٰتِ قَدْحًا ٢

[100:2] Suna masu Qyasta hasken wutan tartsitsi.

فَٱلْمُغِيرَٰتِ صُبْحًا ٣

[100:3] Sa'an nan suna kai hari a lokacin asuba.

فَأَثَرْنَ بِهِۦ نَقْعًا ٤

[100:4] Suna masu razanarwa daga nan.

فَوَسَطْنَ بِهِۦ جَمْعًا ٥

[100:5] Suna shiga har cikin iyakanta a tsakanin jama'ar maqiya.

إِنَّ ٱلْإِنسَـٰنَ لِرَبِّهِۦ لَكَنُودٌ ٦

[100:6] Mutum mai tsananin butulci ne ga Ubangijinsa.

وَإِنَّهُۥ عَلَىٰ ذَٰلِكَ لَشَهِيدٌ ٧

[100:7] Shi mai shaida ne a kan laifinsa akan haka.

وَإِنَّهُۥ لِحُبِّ ٱلْخَيْرِ لَشَدِيدٌ ٨

[100:8] Kuma yana tsananin son abin duniya.

۞ أَفَلَا يَعْلَمُ إِذَا بُعْثِرَ مَا فِى ٱلْقُبُورِ ٩

[100:9] Shin, bai san cewa, wata rana za tone abin da ke cikin kaburbura ba ne?

وَحُصِّلَ مَا فِى ٱلصُّدُورِ ١٠

[100:10] Kuma a bayyana abin da ke cikin zukata.

إِنَّ رَبَّهُم بِهِمْ يَوْمَئِذٍ لَّخَبِيرٌۢ ١١

[100:11] Za su sani, a ranar nan, cewa Ubangijinsu, Mai qididdigewa ne.